Hannu maɗaukaki shi yafi alheri daga hannu maƙasƙanci

Daga Abdullahi ɗan Umar - Allah Ya yarda da su -: Cewa Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce akan minbari, kuma sai ya ambaci sadaka, da kamewa, da kuma roƙo: «Hannu maɗaukaki shi yafi alheri daga hannu maƙasƙanci, hannu maɗaukaki: Shi ne mai ciyarwa (mai bayarwa) maƙasƙanci kuma: Shi ne mai roƙo».

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ambata alahali yana huɗubar akan sadaka da kamewa daga roƙo akan minbari; sannan ya ce: Hannau maɗaukaki mai ciyarwa mai bayarwa shi ne nafi alheri kuma mafi soyuwa a wurin Allah daga hannu maƙasƙanci mai roƙo.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/3599